## Addu'oi da furuci

***Addu'ar tuba***

*Allah Mai kauna, ina furta cewa nayi zunubi, na kuma juya maka baya. Na tuba, na juyo zuwa ga Kristi a matsayin Mai ceto da Ubangiji na. ka gafarta mani barazanas da nayi ta yi wa wadansu, lokutan da nayi kokari in kaskantar ko kuma in wulakanta wadansu. Ka gafarta mani girman kai na. ka gafarta mani dukan lokatan da na ci zarafin wani ko na dora kaina a bisan wadansu. Na rabu da dukan wadannan a cikin sunan Yesu.*

*Allah da Uban Ubangijinmu Yesu Kristi, ina yabon ka domin kyautar gafara da Yesu ya samo a bisan giciye domina. Na yarda cewa ka karbe ni. Na gode maka domin mun sami sulhu da kai da kuma juna ta wurin giciyen. A yau ina shaida cewa ni naka ne (da/diya) kuma magaji na Mulkin Allah.*

***Furuci da yin watsi***

*Uba, na amince da abin da ka fadi cewa ni ba bawan tsoro ba ne, amma ni da ne na kaunar ka. Ina tsinke kowace irin dangantaka da abubuwan da Musulunci ya kunsa wanda Muhammadu ya koyas. Na ki kowanne irin sadaukar da kai ga 'Allahn dake cikin Alkur'ani', ina kuma shaida cewa ina bautar Allah na Ubangijinmu Yesu Kristi ne kadai.*

*Mun tuba daga zunuban da kakanninmu suka aikata wajen mika kai a karkashin danniya ta dhimma da dukan abin da wannan ya kunsa, ina kuma rokon gafararka domin zunubansu.*

*Na soke na kuma tsinke dukan mika kai da na yi, ko wanda kakannina suka yi zuwa ga al'ummar Musulmi.*

*Na yi watsi da danniyar dhimma kwata-kwata hade da dukan ka'idodi da sharuddan ta. Na soke bugu a wuyan da ake yi a cikin al'adar biyan haraji na jizya hade da dukan abin da wannan yake wakilta. Ina soke la'anar nan da al'adar sare kai da kuma mutuwar da wannan yake wakilta.*

*Na furta cewa an kafa yarjejeniyar danniya ta dhimma a bisan giciyen Kristi. An kunyatas da dhimma a cikin jama'a, kuma ba ta da iko ko hakki a bisa na. Ina furta cewa ikon ruhaniya na yarjejeniyar dhimma ya tonu, an kwace makamanta, an yi nasara da ita, an kuma kunyatar da ita ta wurin giciyen Kristi.*

*Na ki kowace irin godiya ta karya ga Musulunci*

*Na rabu da kowace irin tsarguwa*

*Ina tsayayya da kowane irin rudi da kuma karya*

*Na yi watsi da dukan jarjejeniyar da ta hana ni bude baki in shaida bangaskiya ta a cikin Kristi*

*Na yi watsi da dukan jarjejeniyar da ta hana ni fadin gaskiya akan abin da ya shafi danniya ta dhimma da kuma Musulunci*

*Zan yi Magana, ba kuwa zan yi shuru ba*

*Ina furta cewa, 'Gaskiya zata yantas da ni'(Yahaya 8:32) kuma na zabi in yi rayuwa a matsayin mutum mai yanci a cikin Kristi Yesu*

*Ina ki, ina kuma soke dukan la'anar da aka furta a kaina, ko a bisa iyalina da sunan Musulunci. Na ki, ina kuma soke kowace irin la'ana da aka furta akan kakanni na.*

*Na ki, na kuma karya la'anar mutuwa. mutuwa, baki da iko a bisa kai na*

*Ina furta cewa wadannan la'anonin basu da iko a kai na.*

*Ina rungumar albarku na Kristi a matsayin gado na na ruhaniya*

*Ina gaba da ruhun tsorataswa. Na zabi in zama mai karfin hali a cikin Kristi Yesu*

*Na ki dukan magudi da tilastawa*

*Na ki cin zarafi da kuma tashin hankali*

*Ina tsayayya da tsoro. Ina kin tsoron rashin amincewa da ni. Ina kin tsoron rashin dukiya ko wata kadara dake mallaka ta. Na ki tsoron talauci. Na ki tsoron bauta. Na ki tsoron fyade. Na ki tsoron kadaici. Na ki tsoron rasa iyali na. na rabu da tsoron cewa za'a kashe ni da kuma tsoron mutuwa.*

*Na yi watsi da tsoron Musulunci. Na yi watsi da tsoron Musulmi.*

*Na yi watsi da tsoron sa hannu a cikin jama'a da harkokin siyasa*

*Ina furta cewa Yesu Kristi shine Ubangijin duka*

*Ina mika dukan rayuwata ga Ubangiji Yesu. Yesu Kristi shine Ubangijin gidana. Yesu Kristi shine Ubangijin birninmu. Yesu Kristi shine Ubangijin Kasata. Yesu Kristi shine Ubangijin dukan mutanen kasar nan. Na mika kaina ga Yesu Kristi a matsayin Ubangiji na.*

*Na ki yarda da kaskanci. Ina furta cewa Kristi ya karbeni. Shi kadai nake bautawa.*

*Ina tsayayya da kumya. Ina furta cewa na sami wankewar zunubaina a cikin giciyen. Kumya bata da iko a bisana, kuma zan yi mulki a cikin daukaka tare da Kristi.*

*Ubangiji, ka gafarta mani, ka kuma gafartawa kakanni na dukan gabar da muka nunawa Musulmi. Ina tsayayya da gaba da Musulmi da kuma sauran jama'a, ina kuma furta kaunar Kristi zuwa ga Musulmi da sauran mutanen duniya.*

*Ina tuba daga zunubin ikilisiya da kuma inda na mika kaina a cikin kuskuren da shugabannin ikilisiya suka aikata.*

*Ina tsayayya da wariya. Ina furta cewa Allah ya gafarta mani ya kuma karbe ni ta wurin Kristi. Na sami sulhu da Allah. Babu wani iko a sama ko a duniya da zai iya yin karata da laifi a gaban kursiyin Allah*

*Ina furta yabo da godiya ga Allah Ubanmu, ga Kristi wanda shi kadai ne mai ceto, ga Ruhu Mai Tsarki wanda shi kadai ne ya bani rai.*

*Ina mika kaina ga zama shaida mai rai ta Yesu Kristi, cewa shine Ubangiji. Ba na jin kumyar giciyensa. Ba na jin kumyar tashinsa daga matatu.*

*Ina furta cewa ni dan Allah mai rai ne, Allah na Ibrahim, Allah na Ishaku da Allah na Yakubu.*

*Ina furta nasarar Allah da ta Almasihunsa. Ina furta cewa kowace gwiwa zata rusuna, kuma kowane harshe zai furta cewa Kristi Ubangiji ne zuwa ga daukakar Allah Uba.*

*Ina furta gafara zuwa ga Musulmi domin sa hannun da suka yi wajen aikata danniya ta dhimma.*

*Allah Uba, idan ka yarda ka yantas da ni daga yarjejeniyar danniya ta dhimma, ruhun wannan danniyar da dukan munanan dabi'un dake tattare da yarjejeniyar dhimma.*

*Yanzu, ina roko ka ciki ni da Ruhu Mai Tsarki, ka kuma zubo mani dukan albarkun Mulkin Yesu Kristi. Ka bani alheri in gane da gaskiyar Maganar ka dalla-dalla, in kuma yi afani da ita a cikin kowane sashe na rayuwata. Ka bani kalmomi na bege da na rai kamar yadda kayi alkawali zaka yi, ka albarkaci lebunana domin in iya yin Magana da mutane da ikon dake cikin sunan Yesu. Ka bani karfin halin in zama da aminci wajen shaidar Kristi. Ka bani kauna mai zurfi ga Musulmi da kuma marmarin nuna masu kaunar Kristi.*

*Ina furta ina kuma yin roko domin dukan wadannan a cikin sunan Yesu Kristi Ubangijina da kuma Mai cetona. Amin*